**Kungiyar Ƙasar Japon Mai Kula Da Hulɗar da Ƙasashen Duniya**

**Jamahuriyar Nijar Ministan Gidan Gona**

# Puroje mai kula da bincike-bincike don bunkasa ayukkan noma a cikin fadan mu na cikin yankin sahel-Niger



LITTAHIN BADA HORO DANGANCE DA TAHIYAR DA KANAN SANA'O'I A CIKIN KARKARA

*Kungiyar Ƙasar Japon Mai Kula da duk abinda ya shahi Arziki na Tsanwa (J-GREEN)*

**An wallafa wannan littafi karkashin yarjeyjiniyar da aka yi da Kungiyar ADA**

*Watan Discemba 2007*

# ABUBUWAN DA LITTAHIN YA ƘUMSA

## GABATARWA


I. ABINDA YA SA AKA WALLAFA WANNAN LITTAHI ................................ 1

II. GURIN WANNAN LITTAHI ........................................................................ 2

III. ABUBUWAN DA AKE SON CIMMA ......................................................... 2

IV. SANA'A ITA MA MASANA'ANTA (KANFANI)........................................... 2

4.1. YADDA MAI SANA'A YA DACE YA TAHIYAR DA SANA'ARCHI ......... 2

4.2. DANGANTAKA TSAKANI DANA'A DA IYALI....................................... 5

4.3. SANA'O'I IRI – IRI NE ........................................................................... 5

4.4. NAZARI DAN GANO IN SANA'AR NA DA HASKE .............................. 5

4.5. JALLIN SOMA SANA'A .......................................................................... 9

4.6. SANIN KUƊIN DA KAYA YA KAMA ..................................................... 10

4.7. ASUSU (Kyas))........................................................................................ 11

4.8. TUNANIN YIN MASANA'ANTA ............................................................ 12

4.9. BUNKUSA SANA'A ............................................................................... 13

- Takardar asusu ta rana – rana
- Takardar shaida.

## Gabatarwa

Wannan littahi an wallafa shi a cikin tsarin aiki puroje kula da bincike – bincike don bunƙasa ayukkan noma a cikin yankin sahel Nijar (EDOS) don taimaka ma maza da mata masu yin ƙanana sana'o'i a karkara.

## I. ABINDA YA SA AKA WALLAFA WANNAN LITTAHI

Manufar puroje kula da bincike – bincike don bunƙasa ayukkan noma a cikin fadamar na yankin sahel Nijar, ita ce yaƙi da talauci da hamada, tare da raya wuraren da suka sami ayukka na musanman na shigaban ƙasa (Dam baraji da saurensu).

Horo dangantce da tahiyar da sana'o'i na karkara na da ma'ana sosai saboda yana ba mutanen karkara damar gane yadda ake tahiyar da sana'a ko da ta saye da saida albarkatun gona ne. Sana'a abu ce mai mai bunƙasa mutun ko jama'a.

Sana'a aikin ne wanda mutun ko jama'a ke yi don samun riba don a biya wasu daga cikin bukatu.

## II. GURIN WANNAN LITTAHI

Gurin wannan littahi shine ba mutanen karkara ilimin tahiyar da sana'o'i na mutun ɗaya ko na jama'a inda zai iya aunawa da yin ruskwana harakokin shi shi da kanshi.

## III. ABUBUWAN DA AKE SON CIMMA

Abubuwan da ake son cimma su ne:

- Maza da mata mazamna karkarar sun sami ilimi da husa'o'in tahiyar da sana'o'i.
- Mutanen karkara sun lura da hanyoyi na samu taimakon tahiyar da sana'o'i.
- Maza da mata sun fa'inta (gamsu) da ma'anar masana'anta.
- Maza da mata suna da ilimi da husa'ar auna sana'arsu da yadda ya kamata a tahiayr da ita tsap.

## IV. SANA'A ITA MA MASANA'ANTA (KANFANI)

Sana'a aiki wanda mutun ɗaya ko jama'a ke iya yi don ɓinar riba. Idan ana son sana'a ta yi haske sai waɗannan ka'idodi sun cika:

- Nazari sosai don gano tabbat sana'ar za ta yiwu.
- Gano tabbat in za a sami riba.
- Gano (sanin) dokokin kasuwanci.

Abun nuhi shi ne:

- Samun niyya cikakka da kuzari yin sana'a.
- Yin sana'a mai iya jayo riba mai yawan gaske.

### *4.1. YADDA MAI SANA'A YA DACE YA TAHIYAR DA SANA'ARCHI*

Sana'a harakar kasuwa ce kenan ta sha'anin neman kuɗi ce, don haka said a halulluka nagari ga wanda ke yenta.

a) **Kaƙa ne mai sana'a yake**

Mai yi sana'a mutun wanda ke da mahimmanci a cikin harakokin tahiyar da sana'a.

Shi ke da nauyin tahiyar da sana'a da kyausaboda a cimma guri. Bunƙasar sana'a na nan saƙe da niyyar da ka ɗauka wajin yi ta, rashin tsoron hasara, wajen ɗaukar matakkai da sauransu.








1. Nemar shawara ga yan kasuwa.
2. Tuntuɓar na kusa wanda sana'arshi tan a tahiya da kyau.
3. A nemi horo ko ƙarin sani da sana'a ta ci gaba.

b) <u>**Gurin da kawane ɗan kasuwa ke son cimma**</u>

Sana'a abu ce wadda ke son a ce ana da kaya iri – iri saboda a biya ma masu ciniki buƙatar samun abinda duk suke dan, bayan wanan, sana'a abu ce wadda ke ba mai yinta damar:

- Yin arziki ta hanyar samun riba, ajiya, ƙadarori da sauransu.
- Ba waiwa kansa aiki.
- Biya ma iyali buƙatu.
- Mallakar abubuwan da ake nema yi.



Mai sana'ar tuyar ƙosai na ba gurin hin turka rago kuma ga biya kuɗin karatun yaronta.

### *4.2. DANGANTAKA TSAKANI DANA'A DA IYALI*

Sana'a aiki ne wanda ke son taimakon mutanen gida ko wani cau dabam – yana da kyau amma yana iya kowa matsaloli. Don haka ayi hankali saboda bambanta sana'a da iyali. Matsalar gida a magance ta a gida, wirin sana'ar kowa ma aikaci ne da na gida da wanda aka dauko daga waje.



Wani pasinja ba ya son ya biya kuɗin mota saboda direba ɗan garinsu ne, sauran ko sun biya har sun shiga sun zamna. Ya ɓata masu lokaci.

### *4.3. SANA'O'I IRI – IRI NE*

A cikin karkara, ana yin sana'o'i kala – kala. Akwai waɗanda ake yi lokacinsu i, ya kama (noma, kiwo). Ko kuma sana'o'i kamar hayar kayayyaki, gandar ɗiyar itatuwa, aikin ƙarhi da sauransu.

### *4.4. NAZARI DAN GANO IN SANA'AR NA DA HASKE*

Nazarin zai shahi duk fannonin girka sana'ar. Wannan nazari zai buda dammar sanin cikakken yanayin da sana'ar za ta guduna saboda a samu dammar auna ta.

#### a) Fuskar tahiyar da sana'a a ka'idance

Kahin a soma sana'a sai an san:

- Sai an gano in sana'ar ta dace da yanayin wurin da za'a yinta ta.
- Sai wanda zai yi irin sana'ar in ya san sana'ar ko kuma ya san inda zai je don ya sami cikakkun labaru bisa sana'ar saboda ya yi odar kayan irin waɗanda jama'a ke so.
- Wanda ke yin sana'a yana da jalli ko kuma ramce ne zai yi? Kuma wa zai bashi ramce? Ko da yake akwai wata sana'a da ba ruwanta da jammisomawa.
- Su xanene masu zuwa saye?
- Wane wuri ko su wanene waɗanda ake iya saida ma kaya?
- Har akwai wasu masu irin wannan sana'a?

- Wane mataki za a ɗauka?
- Har akwai lokacin da ya hi dacewa da sana'ar?

**b). Kasuwa**

ana nuhi da kasuwa, duka mutane karkara masu bukatar kaya kuma masu halin sayen su, don haka sai ,ai sana' a ya san ko su wanene masayanshi idan aka yi bincike ana iya gano masayan kaya da kuma wasu yan kasuwa masu saida irin kaya daya irin wa,da ake saidawa

Ta haka za a yi ma kansa tambayoyi kamar haka:

- su wa da wanene ke masayan kayana?
- Wane irin kaya su ka hi bukata? Thayonshi, launinshi, kyanshi, kundishi da sauransu
- Farashin da mutane ke iya sayen kayan?
- Ina ne masayan suke? Kuma ina ne suke saba sayayya

Sana'ar bata tahiya da kyau sai da masu saye, don haka mai saye na da mahinnmanci kwarai cikin sha' anin kasuwa

**b.1.) tsarin tahiyar da siyasar kasuwanci**

Tsarin siyasar tahiyar da kasuwanci, shi ne dubara don gano masaya da kuma ire - ire kayan da suke bukata, har ila yau wannan siyasa sai in ta dace da ana samun riba, amma sai an san:

- Wane irin kaya za a saida ?



Tahiru, dan sana'ar saida murhun zamani na na karfe, uwargidan aliyo mai saida kosai na shan matsala wajen hura huta.

- Wane irin parashi za a sa ?



Matar Ambuka na saida kayayyaki iri – iri tana sa ma kowane kaya parashi wanda ya dace yadda da mai karhi da maras karhi na samun rabonshi.

- Wuri sana'a : kaka da kuma

Ina ne ya dace a aza sana'ar don masaya su samu,




Zaben wuri sana'a na da mahimmanci sosai wajen sha' ani sana' a

Nan mutun biyu ne masu sana’ar paci, na farko na bakin hanya amma ba ciniki, na biyu na cikin gareji amma shina samun ciniki

- Kaka ake sanar da masaya da kuma kaka ake jan ra’ayinsu ?






1. wurin cin abici maras tsabta, diyan mai abinci suna damuwar masaya abinci da ba su da wurin zama ma na kirki.
2. wuri abinci tsabtace, akwai mai tamakawa wajen bada abinci, runfa mai kyau da wurin zama mai kyau, masu saye na cin abinci lahiya lau .

### b.2.). Nagartaccen mai saidawa

Gurin duk sana'a , a sayo kuma a saida maza- maza lalle kaya na ƙwarai, parashi mai rahusa da wurin sana'a mai kyau na jayo masaya amma a ƙara sa hali mai kyau kamar fara'a, iya ciniki, hanƙuri da sauransu



Masu sayen abinci na jiran a sa masu abinci, mai saidawa na ta surutu da abukiyarta

### *4.5. JALLIN SOMA SANA'A*

Jalli somawa shi ne Kudin da a ka buKata don a fara sana'a da farko wanda zai bada damar saye kayayyaki ko hayar wuri sana'a da sauransu.

#### a) Kaya waɗanda za a sarrafawa

Kaya waɗan da ake sarrafwa su ne waɗanda daga gare su ina iya yin waɗansu abubuwa idan aka aikata su. Misali: daga wake ana iya a yi ƙosai

#### b) Kayan aiki

Kaya ne waɗanda ake amfani da su ajen sarrafa abubuwa kamar injina da sauransu.

Jalli farko ya kamata a saka a hanya ta ƙwarai kamar:

- sayo kayayyaki mara tsada a cikin locacin da ya dace.
- Sayo kayan aiki masu daɗe wa waɗanda ake samun kayan gyaransu ba da wahala ba.

*4.6. <u>SANIN KUƊIN DA KAYA YA KAMA</u>*

a) <u>Kuɗin da kaya ya kama</u>

Duk abu yana da kuɗin da ya tashi sawa na sarrafa shi ko kuma yadda ya kama idan an haɗa da duk kashe – kashen da aka yi kahin ya zo fagen saidawa.

b) <u>Lissahin kuɗin da kaya zai tashi</u>

Lissahin na bada damar a san ko nawa na kayan zai tashi ko zai kama kahin a tsaida ko nawa ne za a saida shi.




Zuwaira na tunani tahiya kasuwar dabobi dan ta sayo rago, kuma ta na tunanin har ila yau sayen ciyawa, dussa alkama, da kuma maganin kashe tsutsotsin cikin cikin raguna da kuma bitamin.

c) <u>Amfanin lissahin kuɗin da kaya zai kama</u>

1) Sanin yadda kaya ya tashi, yana sa a tsaida parashi wanda za a samu riba.
2) Sani kuɗin da aka kashe na sa a taƙaita kashe – kashe waje sarrafa kaya sai kaya su hito ba da stada ba.
3) Haka ma yana sa a ɗauki matakkai waɗanda suka dace cikin tahiyar da sana'ar.

*4.7. <u>ASUSU (Kyas)</u>*

Sha'anin kasuwa abu ne mai kyau kuma mai wuya. Don haka sai da kuzari da daurewa, shi ya sa sai ana yi ana barin shaida rubutatta ta shiga da hitar kuɗi.

a) <u>Rubutu cikin girgam na shiga da hitar ƙudi</u>

Don haka yana da kyau a zan riƙa rubuta shiga da hita kuɗi saboda haka nan ya hi tsari. Don shaida kuma a zan yin takardun an biya kuɗin kaya ka kuma an amshi kuɗi (resi ko fakatir)
Sai an rubuta :

- nawa ne ya shigo ?
- nawa ne ya hita ?




Malam Karimun, kahinta ne ya zo ya sayi kaya an bas hi takardun sayen kaya (fakatir).

b) Girgam na shiga da hitar kuɗi

Girgam babban tabuli ne in da ake rubuta shiga ko hitar kuɗi.
Ana cika shi kowace rana :

- A rubuta duka cinihin da aka yi da irin kayan da aka saida.
- A rubuta kashe – kashen da aka yi da kuma dalillan da ya sa

*4.8. TUNANIN YIN MASANA'ANTA*

Ana nuhi da masana'anta tsarin kasuwanci nagartacce wanda ba zai kawo hasara ba ko mugunyar faɗuwa. Don haka stari yana da mahimmanci sosai a ciki sha'anin kasuwanci.

*a.)* Samun ra'ayin sana'a tagari

Zaɓin irin sana'ar da mutun za ya yi yana zo mashi ne a kai ko kuma daga buƙatun jama'a ko kuma dangance da kayayyaki da ke nan cikin mahallinshi de sauransu.
Ra'ayin na zo ma mutun, shi kuma mutun sai ya yi mashi fasali mai kyau.

*b.)* Tushen ra'ayin yin sana'a

Tushen ra'ayin yin sana'a suna da yawa. Ana iya amfani da :

- Dag sana'ar da anka riga aka san ta: yarinyar da ta taso a gidansu ana yin sabunin salo?
- Kahohin wasta labaru (tele, radiyo de jaridu).
- Kasuwar baza koli (ana tallar a tele da radiyo da jaridu).
- Bincike don gano irin kayayyakin da jama'a ta hi saye.
- Daga suka ra'ayin jama'a rashin gamsuwarsu dangance daga shigowar sabin kayayyaki.
- Daga tunanin mutun don kawo magani ga wasu matsalolin jama'a.



Malam Abduna kalon sharhi bisa zance kiwon kaji a tele, nan take sai ya yi niyyar yin sana'ar kiwo kaji

### *4.9.* *BUNKUSA SANA'A*

Ya kamata a tahiyar da sana'a yadda za a sami riba. Don haka sai a lura sosai don agane abubuwa ko ayi tsari larwan kuɗi.

Fasali mai kyau na sa a gano abinda ke iya faruwa na gaba a ciki sana'ar.

#### *a.)* **In da ake nuhi a je a cikin lokacin da aka tsaida**

Idan aka yi fasali, ana staida in da za a je. Shi ke sa a san abubuwan da za a yi nan gaba. Misali : Gobe ranar kasuwar gari ce, malama Halima mai sana'ar toya ƙosai ce, ta ɗauki niyyar yin ƙosai na tiya biyu na wake maimakon guda ɗaya da ta saba toyawa.

Dan kasuwa mai tsinkaye na iya kwatamci kamar haka:

- Nawa zai saida a cikin wata shekara ko hiye ?
- Nawa ne kuɗin waken da yake nuhin saya ?
- Kuɗi na hannunshi nawa ?
- ƙaƙa za tsaida parashinshi idan ya biya buƙatunshi masaya kuma ya ci riba.

Lissahin raskwana

Ana yin raskwana tsakanin cinikin da aka yi da kuma kuɗin da kayayyaki suka kama a tsawon kowane wata na shakarar farko sai a gano nan take in ana samun riba ko kuma ana iya samun mastalar kuɗi zuwa gaba. Ana iya lissafa ribar da aka ci.

| Ciniki na kayan da aka saida | - | Kuɗin da kaya ya kaka lokaci saye | = | Riba |
|---|---|---|---|---|

In dai sana'o'i ne irin na karkara ribar da aka gani ita ce ribar duka saboda ba za a hidda wasu kashe – kashe can dadam.

**Misalin raskwana na kwana 7 na sana'ar ƙosai**

| KASHE – KASHE | | | | | CINIKI/KUƊIN ƘOSAI | | RIBA |
|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Sunan kaya | Ma'auni | Yawan kaya | Kuɗin ƙwara 1 | Jimilla | Ciniki rana/rana | jimilla | Riba |
| Wake | Tia | 1 | 450 | 450 | ƙosai | 2 000 | |
| Mai | Litir | 1 | 850 | 850 | | | |
| Gishiri | kulli | 1 | 25 | 25 | | | |
| Tanka | Kulli | 1 | 25 | 25 | | | |
| Kuli-kuli | Kwara | 15 | 5 | 75 | | | |
| Maji | Kwara | 1 | 40 | 40 | | | |
| Itace | Kashi | 1 | 100 | 100 | | | |
| Ruwa | Bokici | 2 | 5 | 10 | | | |
| niƙa | Tia | 1 | 50 | 50 | | | |
| **JIMILLA** | | | | **1 625 F** | | **2 000 F** | **+ 375 F** |

**Riba = Ciniki – kuɗin kaya**

**375 F = 2 000 F - 1 625 F**

Idan aka raskwanar a tsawon sati sai a sami :

- kasha – kasha = 1 675 F x 7 = 11 325 F
- ciniki = 2 000 x 7 = 11 000 F
- riba = 14 000 F – 11 325 F = 2 625 F

Halima mai toya ƙosai za ta sami ribar 2 625 F a cikin sati, a wata ɗaya ko za ta sami :

- **kashe – kashe** : 11 325 F x 4 = 45 300 F
- **ciniki** : 14 000 F x 4 = 56 000 F
- **riba** : 56 000 F – 45 300 F = 10 700 F

A wata mai ƙosai za ta ci ribar 10 700 F, a stawon shekara ɗaya za ta sami :

- **kashe – kashe** : 45 300 F x 10 = 453 000 F
- **ciniki** : 56 000 F x 10 = 560 000 F
- **riba** : 560 000 F – 453 000 F = 107 000 F

Mai ƙosai za ta sami ribar 107 000 F da za ta hidda jallinta, wahalarta da kuɗin canza kayan aikinta waɗanda suka lalace.

*b.)* <u>Amfanin fasali cikin sha'anin sana'a</u>

Fasalin kuɗi a cikin sana'a na da amfani saboda yana taimakawa waje bunƙasa sana'a.

- Yana gwada ma mai sana'a in yana iya cin riba
- Yana nuna ina ne ya kamata a yi ma gyaran fuska saboda abu ya tahi da kyau
- Yana nuna ma'aikacinnan asusu ko manyan bankoki yadda sana'arku take bunƙasa
- Yana nuna shiga da hitar kuɗi a cikin sana'arku.

Don haka ya daidaitu ku yima sana'arku fasali. Fasali sun kasu kashi biyu:

- fasalin saidawa da kuɗaɗen da abubuwa za su kamawa, shina sawa a ci riba
- fasalin kuɗi tsaba: shina sawa hankali ya kwanta don ba za a sami matsalar kuɗi tsaba.

c.) <u>Inda za a samo jalli ?</u>

Bayan an ƙare duka wani nazari an san kuɗin da ake buƙata don fara sana'ar, to ina za a same shi ?










1. An samu jalli ta yanyar adashe
2. An samu jalli ta yanyar ramce
3. An samu jalli ta yanyar taimakon ɗan uwa.

# WASU TAKARDUN CIKON BAYANI

# TAKARDAR SHIGA DA HITAR KUƊI TA RANA – RANA

Ranar ……………………. 200 …

| Sunan kaya | Yawan kaya | Jimilla | |
|---|---|---|---|
| | | Shiga | Kashe-kasher |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| JIMILLA | | | |
| SAURA | | | |

Resi/shaida  mai lamba .............

Jimillar kuɗi ........................................ CFA

Jimillar kuɗi da ta kai : ……………………………………………..... CFA

Dalili ………………………………………………………………………… ………………………………………

Rana …………………………….....

Sa hannun tare da tambarin ma'aikatar.

Resi/shaida  mai lamba .............

Jimillar kuɗi ........................................ CFA

Jimillar kuɗi da ta kai : ……………………………………………..... CFA

Dalili ………………………………………………………………………… ………………………………………

Rana …………………………….....

Sa hannun tare da tambarin ma'aikatar.